(١)

**YAƘI DA CIN HANCI DA RASHAWA DA ƁARNA AIKI NE NA KOWA DA KOWA**

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Kada ka nemi aikata ɓarna a bayan ƙasa, lallai Allah ba ya son maɓarnata)** [al- Ƙasasi: 77], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai ɓarna mummunar ɗabi’a ce da take lalata ƙarfin ɗaiɗaikun mutane, da na ƙasashe, tana kuma zama alaƙaƙai wajen gina ƙasa, da samar da ayyukan raya ƙasa; saboda haka ne ɗaukacin shari’o’i da addinai suka yi gargaɗi akan dukan nau’o’in ɓarna da surorinta, Allah mai girma da ɗaukaka yana faɗi ta bakin Annabi Saleh (AlaiHis Salam) cewa: **(Kada ku aikata ɓarna a bayan ƙasa)** [al- Baƙra: 60], haka ma Mai girma da ɗaukaka yana faɗi ta bakin Annabi Shu’aib (AlaiHis Salam) cewa: **(Kada ku zalunci mutane akan kayansu, kada kuma ku bazama a bayan ƙasa kuna aikata ɓarna)** [Hudu: 85], haka ma Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa ta bakin Annabi Musa (AlaiHis Salam), a lokacin da yake magana da ɗan uwansa Annabi Haruna (AlaiHis Salam) cewa: **(Ka yi gyara, kada ka bi hanyar maɓarnata)** [al- A’araf: 142], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Kada ku aikata ɓarna a bayan ƙasa)** [al- Baƙra: 60], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda yake neman yardar Allah a cikin komai nasa, ya kuma yi wa**

**shugaba biyayya, ya kuma ciyar da dukiyarsa mai daraja saboda Allah, ya kuma sauƙaƙa wa abokan hulɗarsa, ya kuma nesanci ɓarna, to barcinsa da farkensa duka lada ne).**

Ita ɓarna sifofi da surari masu yawa take da su, wadda ta fi hatsari ita ce: karkatar da dukiyar al'umma zuwa azurta kai, da rashin gabatar da ayyukan da suka zama wajibai akan ma'aikaci, da yin alfarma ba tare da cancanta ba, da rashawa, da algushi, duka waɗannan ƙofofi ne na cin haramun, da cin dukiyar mutane ta hanyar ɓarna, Allah mabuwayin Sarki yana cewa: **(Kada ku kuskura ku ci dukiyoyin junanku ta hanyar ɓarna)** [al- Baƙra: 188], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: (**Allah ya tsine wa mai bayar da cin hanci, da wanda aka bai wa cin hanci),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai mutanen da suke kutsawa cikin dukiyar Allah ba tare da haƙƙi ba, wuta tana nan tana jiransu a ranar alƙiyama)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk nama da ya tsiro daga haramun ba zai shiga aljanna ba, wuta ce ta fi dacewa da shi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa**: (Duk wanda ya yi mana algushi ba shi a cikinmu).**

Lallai yaƙi da da dukan nau'o'in ɓarna alhaki ne da ya rataya akan kowa, wanda addini, da zama a ƙasa ɗaya, da rayuwar zamantakewa suke wajabtawa, shi alhaki na addini ya fara ne tun daga gyara zuciya, da tarbiyyantarta akan tsoron Allah, da hararo girma, gami da kwarjininsa a ɓoye da a fili, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Shi yana tare da ku a duk inda kuke, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya game da abubuwan da kuke aikatawa)** [al- Hadid: 4], haka ma Allah mabuwayi yana cewa: **(Lallai da ma can Allah mai sanya ido ne akanku)** [an- Nisa'i: 1],

haka ma dole ne a dasa kyawawan ɗabi'un gaskiya, da riƙon amana, da cika alƙawari da sauransu cikin manyan kyawawan ɗabi'u, shi mumini na gaskiya aikinsa shi ne kawo gyara ba ɓarna ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: (**Ko kuwa za mu sanya waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari su zama sun yi daidai da masu ɓarna a bayan ƙasa ne, ko mu sanya masu tsoron Allah su zama ba su da bambanci da fajirai?!)** [Sad: 28]

Shi kuwa alhakin zama a ƙasa ɗaya yana nufin ƙara ƙarfafa kishin ƙasa a cikin zukata, da zurfafawa wajen ɗaukan nauyi da alhakin da yake kan al'umma wajen kare dukiyar al'umma da kayayyakin gwamnati, da kuma yaɗa saƙafar gaskiya da riƙon amana a cikin ɗaukacin 'yan ƙasa, da kuma hukunta maɓarnata da masu lalata dukiyar al'umma, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya tanadar wa maɓarnata da nau'o'i iri- iri na azaba, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Shi kawai uƙubar waɗanda suke yaƙar Allah Maɗaukakin Sarki da Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa alihi wa sallam) idan suka yi wa tsarin shugabanci da hukunce-hukuncen shari'a tawaye, suka** kuma **cigaba da yin ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar tare hanya da yin fashi da makami, ko ƙwace dukiyoyin mutane: shi ne a kashe su idan sun kashe, a kuma tsire su idan suka yi kisa, suka kuma ƙwace dukiya, a kuma yanke hannayensu da ƙafafuwansu amma a saɓa tsakani idan sun tare hanya, suka kuma ƙwaci dukiya amma ba su yi kisa ba, a kuma kore su daga garin zuwa wani garin na daban, a kuma tsare su a gidan fursuna idan tsoratar da al'umma suka yi kawai. Wannan uƙubar ƙasƙanci ne da wulaƙanci a gare su a nan rayuwar duniya, a lahira kuma suna da azaba mai girma wadda ita ce azabar wuta)** [al- Ma'idat: 33].

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai alhakin zamantakewa yana nufin ƙarfafa saƙafar ƙyamata, da ƙin dukan nau'o'in ɓarna, da kuma al'umma ta sanya ido domin kare rayuwa daga faɗawa cikin hatsarin ɓarna, ta hanyar ƙarfafa ayyukan ma'aikatu da hukumomin addini, da na ilimi, da na yaɗa labarai, Allah mai girma yana cewa: **(Kamata ya yi a ce a cikin waɗancan al'ummomin -da muka halakar da su sakamakon zaluntar kawunsu da suka yi- akwai wasu mutane da ake jin maganarsu, waɗanda suke da addini da hankali, da za su rinƙa hana waninsu aikata ɓarna a bayan ƙasa, inda za su ba su kariya daga azabar da ta same su, amma ba a same sun ba, abin da ya faru shi ne a cikinsu akwai muminai 'yan ƙalilan da ba a saurari ra'ayinsu da abin da suke kira zuwa gare shi ba, sai Allah ya tseratar da su tare da Manzanninsu..)** [Hudu: 116], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(A cikin sunnar Allah da adalcinsa a cikin halittunsa ba ya taɓa zaluntar kowace al'umma daga cikin al'ummomi muddin ta yi riƙo da gaskiya, da kuma rungumi kyawawan ɗabi'u, da kuma yi aiki da abubuwan da za su kawo mata gyara, su kuma kawo wa wasu gyara a cikin al'amurransu)** [Hudu: 117]

Haka ma al'amarin yana buƙatar dole ne a nesanci rufa wa duk wani maɓarnaci asiri, a yi taimakekeniya da hukumomin da abin ya shafa wajen bankaɗo dukan nau'o'in ɓarna, har sai kwanciyar hankali ya karaɗe ko'ina a cikin al'umma, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Misalin**

mutumin da yake tsaye akan iyakokin Allah, da wanda ya auka cikinsu, kaman mutanen da suka shiga cikin jirgin ruwa ne, wasu suka samu wuri a sama, wasu kuma suka samu a ƙasa, sai ya zamana idan na ƙasan suna buƙatar ruwa sai sun biyo ta wurin waɗanda suke samansu, sai suka ce: da za mu huda wani wuri a inda muke, ta yanda ba za mu dami waɗanda suke samanmu ba, idan na saman suka barsu suka aikata abin da suka yi nufi, dukansu za su halaka, idan suka hana su, sai su tsira, sai dukansu ma su tsira).

Ya Allah Ubangiji ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya baki ɗaya daga dukan abin ƙi.